# Kar ku sanya alhariri (siririnsa) ko dibaji, kuma kar ku sha a cikin kofi na zinare ko na azurfa, haka nan kar ku ci a cikin farantansu, don kuwa na su ne (wanda ba muslmi) a nan duniya ku kuma zaku yi amfani da su a lahira

Daga AbdurRahman Dan Abu Laila cewa sun kasance a wajen Huzaifa, sai ya nemi a shayar, sai wani Bamajushe ya shayar da shi, lokacin da ya ajiye ƙwaryar a hannunsa sai ya jefe shi da ita, kuma ya ce: Da badan ni na hana shi ba, ba sau ɗaya ba, ba kuma sau biyu ba - kamar cewa shi ya ce: Ban aikata wannan ba -, sai dai cewa ni na ji annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana cewa: "Kar ku sanya alhariri (siririnsa) ko dibaji, kuma kar ku sha a cikin kofi na zinare ko na azurfa, haka nan kar ku ci a cikin farantansu, don kuwa na su ne (wanda ba muslmi) a nan duniya ku kuma zaku yi amfani da su a lahira".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya hana maza sanya alhariri da dukkan nau'o'insa. Kuma ya hana maza da mata ci da sha a kofinan zinari da azirfa. Kuma ya bada labari cewa su na muminai ne a ranar lahira; domin su sun nisancesu a duniya dan biyayya ga Allah, Amma kafirai to ba su da rabonsu a lahira; domin su sun yi gaggawar daɗaɗasu a rayuwarsu ta duniya dan sun riƙesu, da kuma saɓawarsu ga umarnin Allah.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee